Jigo A Cikin Finafinan Hausa Da Littattafan Zamani: *Ina Aka Dosa?*

Atiku Ahmad Dunfawa

Muhammad Bashir Yusuf

1.0 Shimfiɗa

Adabi shi ne madubin al'umma wanda suke iya dubawa su ga yadda rayuwarsu ke tafiya. Wannan adabi da ake magana yana da rassa, kuma kowane reshe nasa yana da muhimmanci ga al'umma. Rassan adabin guda uku su ne; waƙa da zube da kuma wasan kwaikwayo. Kowane reshe daga cikin uku ɗin nan yana da muhimmanci ga al'umma ta fuskoki masu yawa, kamar faɗakarwa da ilmantarwa da tarbiyantarwa da kuma nishaɗantarwa da haɓaka harshe da kuma adana al'adu. Ana samun waɗannan abubuwa da aka ambata a cikin rassan adabi gwargwadon yadda aka ƙunsa jigogi a cikinsu. Wannan takarda ta dubi yadda jigogin suke a cikin finafinan Hausa da kuma littattafan zamani na nishaɗi (Adabin Kasuwar Kano) daga shekarar 1980 zuwa yau. Ta hanyar duba yanayin waɗannan jigogi ne za a iya ganin shin ci gaba adabin Hausa yake samu ko ci baya dangane da muhimmancin da aka ambata nasa.

2.0 Jigo

Masana sun bayar da ma'anar jigo ta hanyoyi daban-daban, amma idan aka dubi ma'anonin sai a ga duk waje ɗaya suka dosa. Wani masanin cewa ya yi:

> "Jigo shi ne dunƙulalliyar manufa wadda domin ta ne aka haddasa wallafa. Kafin mutuum ya ɗauki alƙalami ya rubuta wani abu, dole ya kasance yana da manufa, to wannan manufar it ace jigo" Ɗangambo (1979).

A wani ƙaulin kuma, cewa aka yi:

> "Jigo na nufin saƙo ko manufa ko bayani ko ruhin magana wanda shi ne ake son isarwa ga masu saurare ko masu karatu ko masu Nazari" Yahya(1979).

Wani wurin kuwa, sai aka ce:

> "Jigo shi ne saƙo ko manufa" Gusau(1988).

Idan aka lura da bayanan masana, za a ga kowane ya ambaci kalmar "manufa". Wannan ya nuna manufar da marubucin littafi ko mai shirya fim ta ƙunsa a cikin littafi ko wasarsa ita ce jigo. Kowane littafin nishaɗi na zamani ko wasar kwaikwayo da aka shirya, yakan kasance akwai nishɗantarwa a ciki, domin wannan nishaɗin ne ke jan hankalin mutane su fahimci saƙon littafin ko wasar, wato a fahimci jigo a cikin sauƙi ba tare da ƙosawa ko gundura ba.

2.1 Jigogin Finafinai Da Littattafan Zamani

Bayanin da ya gabata ya nuna cewa, amfanin finafinai da littattafan zamani na Hausa shi ne ilmantarwa da faɗakarwa da tarbiyantarwa da dai sauransu. Abin tambaya a nan shi ne, waɗannan finafinai da littattafai suna yin wannan aiki? Idan har suna yi, shin waɗanda ake yi dominsu na fahimta? Idan ba su fahimta, to don me? Idan kuma finafinai da littattafan ne ba su yin aiki nasu, to me ya sa? Samun amsar waɗannan tambayoyi shi zai zama mizanin auna matsayin finafinai da littattafan zamani na Hausa a cikin al'ummar ta Hausawa, a iskan nan da ke kaɗawa.

Idan za mu amsa tambaya ta farko muna iya cewa finafinai da littattafan zamani na Hausa ba su yin wannan aiki da ya kamata a ce suna yi. idan ko har suna yi, to lalle ya ƙaranta ko kuma ya karkata a wani ɗan ɓangare kawai. Misali, kusan dukanin jigogin waɗannan finafinai da littattafan sun fi zama a kan soyayya, domin kusan kashi casa'in bisa ɗari (90%) ko ma fiye na jigogin nasu a kan soyayya ne. Soyayya kuwa ba ita ce kawai abin da al'umma Hausawa ke so ko buƙatar a koya musu ba. Idan soyayyar ta yi yawa, kuma ta dasƙare a cikin zuciya, sai ta kashe zuciya ta kuma kashe jikin mai zuciyar.

Dangane da tambaya ta biyu kuwa, idan har masu shirya finafinai da wallafa littattafan zamani suna ganin suna kawo waɗancan muhimman abubuwa a cikin shirye-shirye da wallafe-wallafensu, to lalle ko ba su saka su ta hanayr da waɗanda ake yi dominsu za su fahimta su yi amfani da abin ba. Duk abin da al'umma suka fi fahimta a ciki bai wuce soyayya ba, domin ita aka nuna yanayinta a cikin finafinan da littattafan.

A ɓangaren tambaya ta huɗu yana yiwuwa mu ce, ƙila kasancewar shirya finafinai da littattafan abu ne mai buƙatar kuɗi, to dole a duba hanyoyin samun su. Kawo wa samari da 'yan mata irin abubuwan da suke so a cikin finafinai da littattafan zai sa a samu kasuwa wadda za ta bayar da kuɗi ƙila ga alama ta nan ne hannu ke ƙwace wa masu shirya waɗannan finafinai da littattafai har su shigo da abubuwa masu kawar da hankalin mutane daga fahimtar wani saƙo a cikinsu (idan akwai) face soyayya kawai. Ta hanayr dubawa, sai a ga kamar jigogin finafinai da littattafan zamani na Hausa sun kasance ne a kan soyayya da zamantakewar kiyoshi da kuma neman magani. Wannan ya sa wasu masana suke

ganin shagaltarwa finafinan da littattafan ke yi ba faɗakarwa ba, Al-Kanawy, A. S. (2004).

2.1.1 Soyayya

Soyayya ita ce ƙaunar da ke wanzuwa tsakanin wani abu da wani. Soyayyayar da ake zance a nan ita ce irin wadda ake samu tsakanin jinsin maza da na mata. Jigon soyayya shi ne jigon da ya fi yawa a cikin finafinai da littattafan zamani na Hausa. Kusan da wuya a sami wani littafi ko wani fim wanda ya fito a cikin wannan tsari wanda babu soyayya a cikinsa. Wani lokaci sai ya kasance an gurɓata saƙon ta hanyar shigo da wasu abubuwa ko al'adu waɗanda ba a saba da su a cikin al'ummar Hausawa ba. Misalin wannan shi ne, kamar rawa da 'yan mata, ko ɗaukar yarinyar a tafi yawon shaƙatawa daga ita sai saurayi. Wani lokaci kuma, sai a nuna yara na yi wa iyayensu tsageranci idan suka gilma masu ga sha'aninsu na soyayya. Sai a nuna yarinya na gaya wa ubanta maganganu gates-gatse saboda ya ce ba za ta auri wanda take so ba, a maimakon a nuna bin wasu hanyoyi na rarrashi da kamun ƙafa domin shawo kan lamarin. Wani lokaci kuma sai a nuna yarinya ta ɗauki wani mataki mai halaka ta, kamar ƙona kai ko makamancisa, domin ta sami biyan buƙatarta. Me ya sa ba za a nuna yin haƙuri ko kuma bin hanya ta limana domin samun biyan buƙata ba? Shin ya kamata samari a irin matsayin hankalinsu su da 'yan mata a riƙa nuna masu irin waɗannan hanyoyin?

2.1.2 Zaman Kiyoshi/Kishiyoyi

Kishiyoyi jam'in kishiya ne, wato matar da ke auren miji ɗaya tare da wata matar. Shi ma wannan jigo mai nuna zamantakewa tsakanin kishiyoyi yana yawan fitowa a cikin waɗannan finafinai da litattafai. Ana yawan nuna wannan jigo ne ta fuskar kawo irin ƙulle-ƙullen zamba da ake samu wasu kiyoshi na yi wa 'yan uwan zamansu. Kawo irin wanann jigo na burge yawancin matan aure da kuma ba su tsoro da sa masu tsananin ƙyamar kishiya. Shin ko masu shirya finafinai da mawallafa littattafan zamani suna sane da cewa da yawa wasu mata da 'yan mata kan koyi irin waɗannan makirce-makirce daga finafinansu da kuma littattafansu? Idan ba su sani ba to su sani. Ana sane da cewa, koyaushe ana nuna mai wannan hali bai yi nasara ba daga ƙarshe, amma duk da haka, ba a lokacin da ta aikata cutar sakamakon ke zuwa ba sai daga baya, wato bayan ta sami nasara ta ɗan lokaci. Da yawa akwai masu ra'ayin su cutar ko da cutar za ta dawo masu daga baya ba su damu ba idan dai sun sami damar aiwatar da wata dabara ta makirci wadda ta biya bukatarsu ta lokacin. Daga nan ne wasu mata za su koya su kuma aiwatar.

Me zai hana a riƙa kawo zaman lafiya tsakanin kiyoshi koyaushe da irin ribar da ke ciki, a kawar da kai daga abin da yake da muni ko da kuwa akwai shi domin gudun yaɗa shi a cikin al'umma. Duk abin da aka shigar a fim ko a littafi, ba

wuya zai yaɗu ya game ƙasa. Hausawa kan ce, 'miyagun kaya a bi dare da su', wannan kuwa domin gudun kada sauran jama'a su gani.

2.1.3 Neman Magani

Neman magani shi ne irin huldar da mutane kan yi da bokaye da malaman tsibbu da nufin samun taimakon magance wata matsala ko samun biyan wata bukata ta hanyar aiwatar da wani surkulle da masu neman magani suka yi imani da shi. Neman magani ga kishiya ko wasu masu takara na yawan fitowa a cikin waɗannan finafinai da littattafai. Wanann wani tsohon yayi ne, wanda ya kamata a ce an wuce shi a halin yanzu. Nuna samun biyan buƙata ta hanyar neman magani abu ne mai kashe zuciya ya hana jajircewa ga neman biyan bukata ta hanyar da ta dace, musamman idan aka taras da jahilai. Me zai hana a nuna wa mutane yin aiki tuƙuru a matsayin sanadarin samun biyan buƙata. Ya kamata a waɗannan shekaru na wayewar kai ya zam duk abin da za a nuna wa mutuum a cikin fim ko a saka masa cikin littafi ya kasance abin da mutuum ke iya yi ne a zahiri ta hanayr amfani da hankali da kuma ƙarfi, ba tare da saka wani aljani ko siddabaru ba. Haka shi zai taimaka wa masu kallo ko karatu su iya koyi da abin da suka kalla ko suka karanta. Idan abu ya kasance na aljannu ko siddabaru, ba wani ƙoƙari da mutuum zai ji yana iya yi ya kai wannan matsayi domin ya riga ya san abin ya fi ƙarfinsa. Idan aka nuna mace ta je wurin boka ta sami biyan buƙata, to an bai wa mai kallo zaɓin ko dai ta je can ta sami biyan buƙata ko kuma ta yi haƙuri ta ba da kai bori ya hau. Kamata ya yi a nuna mace ta sami biyan buƙata a gidan mijinta tsakaninta da shi ta hanayr kyawawan halayenta da ɗabi'unta da tsafta da sauran irinsu waɗanda a zahiri suke jan hankalin namiji zuwa ga matarsa kuma mata suke iya aiwatarwa ba tare da boka ko malamin tsibbu ba.

3.0 Buƙatun Jma'a

Akwai abubuwa da yawa masu ci wa jama'a tuwo a ƙwarya a halin yanzu, waɗanda ya kamata a ce masu shirya finafinai da wallafa littattafan zamani sun mayar da hankali a kansu. Waɗannan abubuwa sun haɗa da cin hanci da rashawa, da wayar da kan mutane game da ayyukan gayya da kula da muhalli da kiwon lafiya da tsaron gaskiya da makamantansu waɗanda al'ummar Hausawa ke ɗokin ganin wanzuwarsu tsakanin jama'a. Saka waɗannan jigogi a cikin finafinai da littattafan zamani zai taimaka wa al'ummar Hausawa, domin sai da su kowace irin al'umma ke samun ci gaba. A halin yanzu, kowa na sane da yadda al'ummar Hausawa ke ƙishin waɗannan abubuwa.

3.1 Cin Hanci Da Rashawa

Ana iya daƙushe ƙarfin cin hanci da rashawa a cikin zukatan samari da 'yan mata ta hanayr rage yin amfani da ƙasaitatun kaya ga tauraro/tauraruwa/taurari. Misali amfani da ƙasaitattar mota ga wanda yarinya ke so, ko amfani da ƙasaitaccen

gida, ko kuma wasu ƙasaitattun kayan ƙawa ga tauraruwa. Yin haka na sa saurayin da ko yarinyar da ke kallo ko karatu su ji sai suna da irin waɗannan kayan ƙasaita suke iya burge masoyansu, ko kuma a ƙalla su yi shawar kasancewa haka nan ɗin. Wannan na sa a hankali son jin daɗi da haɗamar tara abu su yi gida a cikin zukatan samari. Haka ma nuna facaka da kuɗi a lokacin bukukuwan aure ko wasu irinsu yake gurɓata zukatan 'yan kallo ko masu karatu. Son gina manyan gidaje da shiga ƙasaitattun motoci da sayen sarƙoƙin zinari da watsi da kuɗi a lokacin buki suna cikin abubuwan da ke ɓata tarbiyar matasa a ƙasar nan. Ci gaba da nuna su a cikin finafinai da littattafai na ƙara rura wutar gurace-gurace, wadda ita ke jawo aikata rashin gaskiya domin cika guri. Zai fi kyau a riƙa kushe wa jama'ar da aka san sun yi ƙauri ga cin hanci ana nuna aibin haka, tare da jawo hankalin mutane a kan rage son aikin ƙasaita. A riƙa kula da karin maganar nan mai cewa: "Bakali kowa ya kashe ka ba ya kirari".

3.2 Ayyukan Gayya

Mutane a ko'ina ba za su sami cigaba ba sai sun san daɗin yi wa kansu ayyuka masu amfanisu su da kansu. Ga al'adar ɗan'adam, duk abin da ya sa hanuu ga samar da shi ya fi jin ciwon lalacewarsa. Masu shirya finafinai da mawallafa littattafan zamani na iya cusa wa samari wannan ɗabi'ar ta hanyar finafinansu na soyayya. A maimakon a nuna yaro ya fito daga ƙauye ko daga wani gidan talakawa ya yi ilmin zamani, ya sami aiki, ya yi ƙaton gida da ƙatuwar mota, sai a kauce wa haka, domin zai saka kwaɗayin waɗannan abubuwa ga samari masu karatu idan sun ƙare nasu karatu, wanda zai ruruta wutar cin hanci.

Kamata ya yi a nuna saurayin ya koma ƙauyensu bayan kammala karatu ya jawo hankalin matasa sun kafa wata ƙungiya suna samar da abubuwan more yayuwa ga jama'arsu. Ko a nuna ya je wata unguwa tasu ya yi irin wannan aiki. Daga nan sai a nuna wani farin jini da ya samu sakamakon wannan aiki da yake yi wa jama'a. Ana ma iya nuna wata budurwa (ɗiyar sarki ko wani mai kuɗi) ta ce tana son sa. Ta haka sai a kawar da hankalin matasa daga kwaɗayin tara abin duniya ta kowane hali, su fita batun manyan gidaje da motoci, su fi damuwa da kwarjini da ɗaukaka a cikin al'umma.

Ko a nuna saurayin da ya sami ilmi yana taimaka wa jama'arsa wajen ƙwato haƙƙinsu daga azzaluman shugabanni da mawadata ta yadda haka zai sa ya sami karɓuwa ga jama'arsa ya yi farin jini a cikinsu kamar yadda abin yake a ɓangaren ƙarshe na littafin *So Aljannar duniya* na Abdulwaheed (1980).

3.3 Kula Da Muhalli

Kyakkyawan muhalli babban abu ne ga rayuwar ɗan Adam wajen kyautata rayuwa da kuma samun abin masarufi. Ya kamata masu shirya finafinai da littattafan zamani su riƙa tsalma jigogi irin waɗannan a cikin shirye-shiryensu.

Wannan ya haɗa da jawo hankalin samari ga dasa itatuwa ko bishiyoyi da kuma rage sare waɗanda ke akwai, da rage farautar namun daji manya da ƙanana. Ana iya saka wannan a cikin finafinai da littattafan soyayya ta fuskar kawo alfanun abin, da kuma cutar rashinsa. A riƙa yi ana haɗawa da maganganu masu shiga rai, kamar yin santi a lokacin da masoya suka zauna ƙarƙashin wata bishiya suka ji sanyin inuwarta. Haka kuma idan suka shiga wani daji ya ba su shawa, ko suka kalli wasu namun daji. A irin wannan loakci sai a kurɗa a saƙon da ke da alaƙa da dashen itatuwa ko hana sare su ko hana farauta. Ta haka sai saƙon ya shiga zuciyar samari, sai a taras kuma ya yi tasiri.

3.4 Kiwon Lafiya

"Lafiya uwar jiki, babu mai fushi da ke". Saka jigogin kiwon lafiya a cikin finafinai da littattafan zamani yana da muhimmanci ƙwarai ga kyautata kiyaye lafiyar al'ummar Hausawa. A maimakon damuwa da nuna asibiti da rashin likitoci ko likitocin buge a wasu asibitoci masu zaman kansu, kamata ya yi a riƙa lurar da mutane yadda za su tsare lafiyarsu. Ana iya yin haka ta hanyar nuna alfanun share gida da tsaftar kici da kayan dafawa da kuma zuba abinci da yi wa yara wanka da kula da kwashe kwata da hana cuɗanya da masu curutan da ake iya ɗauka musamman a tsakanin yara (kamar baƙon dauro da tarin shiƙa). A riƙa yi ana tsarma maganganu masu irin wannan dangantaka a cikin littafi ko a lokacin nuna fim. Yin haka zai taimaka a sami al'umma mai ƙoshin lafiya. Ana iya yin haka ta hanyar nuna mata suna aikin abinci ko shara , ko yara matasa suna taimaka masu tare da jejjefa maganganu masu alaƙa da abin da ake son koyarwa a lokacin gudanar da aikin.

Sai dai za a yi hattara da kayan da za a yi amfani da su a wajen irin wannan nuni ko irin gidajen da za a nuna domin kada a kawo ƙasaitattu irin waɗanda mafi yawan jama'a za su ga kamar ba da su ake zancen ba. Ta wajen abincin ma a guji kawo mai tsada, amma a kawo mai gina jiki, kamar wake ko alayyafu ko ɗan kifi ko nama ba mai wuce wuri ba. wannan ita ce hanayr da Malam Abubakar Tunau Mafara ya bi wajen wallafa littafinsa na *Wasan Marafa* (Mafara,1954).

3.5 Tsaron Gaskiya

Gaskiya dokin ƙarfe. Tsare gaskiya shi ne sirrin ɗaukaka da ci gaban al'umma. Idan babu tsaron gaskiya, sai ka taras babu ci gaba ga al'umma, kuma ko akwai shi sai a taras ga wasu 'yan ƙalilan yake, kamar halin ƙasarmu a yanzu. Ya kamata, duk jigogin nan da aka ambata baya, a riƙa tsalma fa'idar tsaron gaskiya ga taurarun da za su aiwatar da wasannin. Haka kuma masu aiwatar da wasannin su kasance suna kwatanta tsaron gaskiya a rayuwarsu ta zahiri, domin ƙara tabbatar wa masu kallon su ko karatun su cewa da gaske suke yi. Yin haka ba

shakka zai taimaka a sami matasa masu nagarta da za su iya riƙe al'ummarsu, su taimaki ƙasarsu ta sami cigaba mai ɗorewa.

4.0 Naɗewa

Ba shakka, jigo shi ne ruhin kowaɗanne shirye-shirye da za a gabatar ga al'umma ya Allah a wasance ko a waƙe ko zube. Abu ne mai matuƙar muhimmanci a kula da buƙatun jama'a wajen zaɓen jigogin da za a yi amfani da su a cikin finafinai da littattafan nishaɗi na zamani.

Haƙiƙa jigogin soyayya jigogi ne masu farin jini musamman ga mata da matasa, amma duk da haka ana iya shigar da waɗannan jigogi da na ambata tare da na soyayya a cikin finafinai da littattafan zamani a lokaci ɗaya. Maƙalar ta nuna hanyar yin haka ta saka saka taurarun ko da masoya ne su riƙa aiwatar da jigogin tare da soyayya tasu. Idan aka yi haka, an kashe tsuntsu biyu da dutse ɗaya. An yi soayya an yi faɗakarwa. Duk da yake ana son samun kuɗi domin ci gaba da samar da waɗannan finafinai da littattafai haka kuma ana son ci gaba da kyautata ɗabi'un al'umma.

Wani abu da takardar ta ambata shi ne rashin shirya finafinai da littattafai irin na yara, domin daga nan ne ake fara tarbiyya kuma daga nan ne ake barin ta. Lokacin da mutuum ya kai shekaru goma sha takwas da miyagun gurace-guracensa, da wuya a kawo masa wani abu da zai raba shi da su. Idan ko aka fara tun yana yaro, sai ya tashi ba da su ba balle a yi wahalar raba shi da su. Rashin kula da yara wajen tsara musu nasu finafinai da littattafai da waƙoƙi masu cusa ɗa'a, shi ya sa ake ta ƙoƙarin gyara ɗa'ar al'umma abu na faskara, domin ba a faro daga tushe ba. Idan yara suka kyautu, sai a wayi gari ba wata mugunta, domin su ne manyan gobe. Da fatar masu shirya finafinai da masu wallafa littattafan nishaɗi za su kula da buƙatun al'umma haɗe da yara domin taimakawa a sami ingantattar al'umma.

Wasalam

Manazarta

Abdulwaheed, H. M. A. (1980). *So Aljannar Duniya,* Zariya: Gaskiya Corporation

Ahmed, U. B. (1985). *Nau'o'in Wasannin Kwaikwayon Hausawa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press

Al-Kanawy, A. S. (2004), "Finafinan Hausa: Faɗakarwa ko Shagaltarwa" a cikin *Hausa Home Video Technology, Economy and Society,* Kano: Centre for Hausa Cultural Studies in Conjuction with Adamu Joji Publishers

Cibiyar Nazarin Hausa (1977). *Waka A Bakin Mai Ita.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company

Dangambo, A. (1984). *Rabe-raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Bahaushe.* Kano: Triump

Hashimu, M. (ND). *Soyayya Da Rayuwar Aure A Musulunci.* Kano: Al-wafa Printing &Publishing

Mafara, A. T. (1949). *Wasan Marafa.* Zariya: Gaskiya Corporation

Maƙarfi, S. (1970). *Zamanin Nan Namu.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company

Malumfashi, A. (1985). *"Asali Da Haɓakar Rubutattun Wasannin Kwaikwayo Na Hausa."* Kundin digiri na biyu, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Sani, A. A. (1993). *Idaniyar Ruwa.* Kano: Bamos